

# DOMIN KA KAWAI!

Yafi shekaru dubu biyu da suka gabata, an sami farin –ciki mai girma a samaniya sa, anda malaiku sun yi murna da sujada agaban kursiyin Allah domin babban shirin kamna da Allah ya  tanada wa duniya (fansa da kubutarwan mutum ta wurin Dansa Yesu Kristi). Wannan murna da farin- ciki mai girma ana ta maimaita shi duk lokaci da wani ko wata ta karbi bayaswan Allah mai girma na ceto. Ko ka tabba karbon kyautar Allah na ceto?

Bayan fadiwar Adamu mutum na farko, wannan ta sa zunubi ta shiga duniya da sakamakon mutuwa. Allah na da shiri domin ya mayar da mutum zuwa ga rayuwar madawamin rai. Domin a cimma wannan buri (shiri) Allah ya aiko da Dansa Yesu Kristi cikin duniya domin ya dauke matsayin mutum na kasawa zuwa ga cikaken madawamiyar ceton Allah. Ya yantar da mutum akalkashin sarauta da ikon Ibilis. Yesu yace: “Gama Allah yayi kamnar duniya kwarai da gaskiya (har) ya bada makadaicin (Mai daraja) Dansa, domin dukan mai bada gaskiya gare shi (gaskanta, jingina gare, dogare gare) shi ba za shi lalace ba (zo ga hallaka; ya bata) ammayana da rai (Madawami; har abada) (Yahaya 3:16). Yesu ya bayyana manufar zuwansa a cikin duniya, Yace “… Na zo domin su sami rai su kuma sami shi a yalwace (cikakkiya, ta cika tana zubuwa)” Yahaya 10:10.

Bugu da kari, domin a kamala shirin ceton mutum, Yesu Almasihu ya zo cikin duniya, yayi rayuwa kamar mutum, ya sha azaba ya kuma mutu domin ya dauke nauyin zunuban yan adam. Nassi ta shaida mana cewa Allah yayi fushi da zunubi da sakamakonsa da yana kan Yesu Kristi amadadin mu. Ishaya 53: 4 ya ce: hakika ya dauke bakin- cikin mu, da kurakurenmu, muna tsamani a zaba da wahalarsa hukunci ne da Allah yake yi ma sa” Wannan shine abinda kowane mai zunubi zai fuskanta.  Yesu Almasihu baya sha wulakanci domin zunubi da yayi ba; gama ba shi da ko laifi ko kadan- shi cikkakene!

Amma ya dauke zunuban mu akansa da rashin karfinmu ya giciye su akan giciye ta wurin mutuwar sa. A rana ta uku, Yesu ya tashi da rai, wannan alamar nasaransa akan shaidan, zunubi da kuma mutuwa. Yana son (dukan wanda, ko da menene da ya aikata) ya bada gaskiya, ya karbi Yesu Kristi ya zama ubangiji da mai Ceto, zaya kubuta daga fushin Allah. Amma wadan da su ki bada gaskiya ga Yesu Almasihu, zasu sha azaba na mudawamin mutuwa da Ibilis domin zunubansu. Hanyar sami ceto sai ta wurin bada gaskiya ga Yesu Kristi shi kadai (Yohanna 3:16).

Dukan abinda Yesu yayi ba domin kansa ba amma domin mu ne. Ba shi da zunubi ko aibi. Mutum ne mai aibi ta wurin rayuwar zunubi. Amma Yesu Almasihu ya dauki matsayin mutum ta wurin aiki Ceto da yayi. Ya dauke matsayin mu domin mun dauke gurbinsa na adalci. A batun adalci, duk lokacin da muna yin koyi da Yesu Almasihu, muna shan wahala

tare da shi, mun mutu tare da shi, an bisne mu tare da shi, muna ci abinci tare da shi, a yanzu kuma muna zama tare da shi a cikin samai, wuri mafi daukaka gaba da ikoki da mahukuntan mulkin duhu (Afisawa 1:21-26). Lokacin da Yesu Kristi ya ke akan giciye, ya dauke dukan zunuban yan adam akansa. Kazalika, duk lokacin da aka maya haifuwar mu, mun zama sabuwar halita cikin Kristi, kuma mu yayan Allah ne. Mun yi nasara akan shaidan har abada; shartan ya rasa iko akan duk wanda an maya haifuwarsa: sabuwar hallita da Allah ya bada ransa domin shi, yana da nawayar yayi rayuwar tsarki! Mai rayuwar adalci da tsarki yana rayuwar cikin ikon Allah, ya fi karfin yin rayuwar cikin zunubi. Yana da nasara akan ciwo da shaidan.

Yesu Kristi bai kyautu da ya sha wannan azaba ba, domin ya kasance a cikin kyakyawan zumunta tare da Allah Uba, amma yayi wannan domin mu, baya sha radadina abanza ba. Ka cancaci jininsa mai daraja- wannan shine tamaninka na gaskiya. Zaka iya sami wadan nan albarku lokaci da Yesu ya zama mai Ceto da ubangijin ka. Idan ba ka karba kyautar Allah na Ceto ba, ina gayyatar ka ka yi wannan adu'a tare da ni- ka fadi kalmomin nan duk idan ka ke, ka kuma furta su da banyaskiya:

*"Ya Allah, Na gode maka domin ka bada Dan ka Yesu Kristi ya mutu domin zunubai na, ya mayad da ni magadan madawamiyar rai maimakon mutuwar har abada. Na furta cewa Yesu Kristi shine ubangiji da mai ceto na; Na bada gaskiya cikin zuciyar ta cewa Yesu ya tashi daga matatu domin in barata. Bisa ga maganarka, na furta cewa na sami ceto? An maya haifuwar na, yanzu ina da rai madawami. Ina rokon ka, ka cika ni da Ruhun ka mai Tsarki, ka kuma taimake ni in kasance acikin shirin madawamin rayuwarka. Na gode maka Uba cikin sunar Yesu Amin!"*

Ina taya ka farin ciki! Maraba da zuwa cikin iyalin Allah! Yanzu kai sabuwar hallita ne. yana da muhimmanci ka sami Littafi mai Tsarki, ka rika karantawa da adua kullayomi ga Uban ka na sama. Ka rika sujada da ikklisiya da ke koyas da Littafi mai Tsarki. Zaka iya ka rubuto mana domin mun taimaka da takardu da zasu karfafa bangaskiyar ka cikin Kristi Yesu.

---

Ka tuntube mu a wannan adirshi ko ko ka buga mana waya kamar haka:

**LIFE COMMISSION MINISTRY**
+23480-27502374, +23470-32138935, +23480-59153304
P. O. Box 8272, Anglo-Jos, Plateau State, Nigeria
www.lifecommission.org / lifecommission@yahoo.com